




# ROBAN MAHAIFA



Anan ana iya ganin wata ma'aikaciyar, jinya tana tadi da wani mutum da iyalinsa suna dawowa daga gona.



Malamar asibiti tana gaya wa Maigida da Uwargida labarin wani abu wanda akan iya sawa a cikin mahaifa don ya hana yin ciki, Maigida ya nuna sha'a warsa.






Uwargida tayi shawaran ta tafi asibitin da ake shirya tsarin iyali.




A dakin shan maganin ne ma'aikaciyar jinya ke nunawa matar inda mahaifa take a jikin mutum, da kuma inda ya kamata a sanya roban mahaifa.






Ma'aikaciyar junyar tana yiwa matar bayanin cewa akan sanya roban mahaifa.




Sai ma'aikaciyar jiyyar kuma ta baiyanawa matan irin halaiyar da za ta ji bayan dan lokaci kadan da sanya roban mahaifa a jikinta. Ta kuma tabbatar wa matar babu wasu wahaloli da zasu dameta game da saka roban.





Ma'aikaciyar jiyya na sanya roban matunci a cikin mahaifar mace da kuma wata ma'aikaciyar tana taimaka mata. Duk dai sanyawar bata daukar fiye da minti biyar.




Lallai ne mai anfani da wanna roba ta rika tura yatsanta a gabanta ko wane wata bayan ta gama wanki don ta tabo zaren, in kuma ta ji zaren ya nutse sai ta kama hanyar asibiti don a duba a kuma tabbatar roban na nan dan daram a inda ya kamata.






Da sanyawa mata roban matuncin sai ta kama hanyar gida cike da farin ciki—ga kuma katinta na asibiti rike a hannunta.



Sai kuma ta ci gaba da aiyukanta na yau da kullum kamar yadda ta saba.






Wassu mata bayan an saka musu wannan roba sukan sami rashin jin dadi a mararsu, ko su rika'ganin digon jini ko kuma jini mai yawa, wannan babu damuwa, don zai daina bayan watanni uku. To amma a inda mace ta fuskanci zazzabi da ciwon mara ko yoyon farji, to, sai ta komo asibiti don neman shawara, da taimako.




Idan matar ta sami daurewar mara, tana iya amfani daruwan dumi tagasa maranta don taji sauki. Tana kuma iya hadiyar kwayar aspirin don rage zafin ciwon.





Maigida da Uwargida sun kasance cikin farin ciki. Bayan sun dan huta, sai suka yi shawara ya kamata su sake haifuwa.




Saboda haka Uwargida ta tafi da karamar yarta don ta raka ta asibiti a fitar mata da roban daga mahaifarta.





Ma'aikaciyar jiyya ta cire mata roban daga jikinta kuma ta jefar. Cirewar bashi da zafi kuma yakan dauki'yan mintoci kadan.



Iyali sai farin ciki, ga Uwargida da wani ciki bayan da na karshe ya girma. Da zaran an cire wanna roba sai ciki.



PL-NGA-84

Planned Parenthood Federation of Nigeria